# Manzon Ubangiji Allah

**Tarihin**

# Fasta Habila Adda Angyu

**Farkon Fasta na**
**Christian Reformed Church of Nigeria**
**(CRCN)**
**A Wukari, Jihar Taraba**

**Daga Hannun**

**Dr. John/Jan H. Boer**

********
******************
********

# Manzon Ubangiji Allah: Tarihin Fasta Habila Adda Angyu,

**Copyright c 2011 Dr. John/Jan H. Boer**

**An wallafa litafin nan don a tuna da bautar da Fasta Habila Adda Angyu ya yi a kasar Wukari da kewayenta a hannun CRCN, wato Christian Reformed Church of Nigeria. Wanda ke da bukatar kofuna domin shi ma ya girmama Fasta din nan, na ba da izini ya buga wasu kofuna na littafin. Sai kada ya sake wani abu a cikin littafin, ko diga daya ma, ban da izinin mawallafin takardar. Inda bukatar gyara sai a nemi Dr. Boer a**

**< www.SocialTheology.com > ko kuwa a < boerjf@hotmail.com >.**

**Babi na Farko**

**ASALIN HABILA ADDA**

## *Gabatarwa*

Ya dace da mu Kirista na zamanin yau, wato na shakarar 2011 zuwa gaba, mu san kuma mu gane da zafin tsananin da su iyayenmu ko kuwa su kakaninmu na farko cikin Ruhaniya suka sha dominmu mabiyansu mu sami cikakken ceto cikin Macecinmu Isa Almasihu. Yawancinmu na zamanin yau mun karbi Bisharar Isa da araha, ba tare da shan tsanani ba. Wadansunmu Kirista na yau mukan rena su tsofoffinmu cikin Bishara. Wai ba su san komai ba; su mutanen da ne, marasa ilimi, marasa karatu ma, wato jahilai ne su.

A yau haka din nan mu Kirista da yawa mun je makaranta, muna da satifikat da digiri iri-iri har ma da sunan "Dr." Amma irin karantun da yawancinmu muka yi ba na ilimi na gaskiya ba. Kada mu rudi kanmu cewa satifikat namu ko kuwa Dr. namu ilimi ne da kuma mu masu hikima ne na zamani. Karatu namu da digiri namu na yau, ai, na neman kudi ne kurum. Im ba kudi ne kake nema ba, sai an rena ka ne kurum, ba a ganka da daraja ba.

Fasta Habila da matarsa, wato Adisa, ba su je makaranta ban da na fasta ba. Ba su ji Turanci ba sam, sai yaren Jukunanci da na wasu makwabtansu. Amma dai suna da wata hikima irin na Ruhu Mai Tsarki wanda karatu a makaranta ba zai kawo maka ba. Nasu ilimi ne na ainihi, haske ne na gaskiya. A yau haka mu Kirista muna jin dadi ne kawai ckin tafarkin Ubangiji; ba mu san tsanani ko shan asaba domin Bishara ba. Amma kafin zaman Kirista a Wukari ya kai haka, shi Habila din nan da matarsa da wasu tsofoffi suka sha tsanani na gaske. Ya kamata mu 'yan zamanin yau mu gode ma Allah Madaukin Sarki yadda Shi Ya tanada wasu masu Bishara wadanda suka shirya mana hanyar Isa Almasihu daidai da shi Yohanna Mai Yin Baftisma cikin Littafi Mai Tsarki. Da ba domin Fasta Habila da irinsa ba, da mai yiwuwa ne mu Jukunawa muna cikin tsafi na da har yanzu, cikin tsohon jahilci da na duhu, da duniya ta wuce mu, ta bar mu a baya.

## *Asalin CRCN*

Littafin nan batun wani Fasta da wata ikilisiyar da suke cikin garin Wukari, a kudancin jihar Taraba, kuma kudancin kogin Benue kusa da jihar Benue, kuma kudancin jihar Plateau. ‘Yan kasa na ainihi su ne Jukunawa wadanda aka san su kuma da suna Kwororofawa. Da wata kabila ce mai girma wadda ta yake su Kanawa a wasu karne a can baya. Amma ban da su Jukuna kuma ga ‘yan Tiv da Chamba a kasarsu. Har yanzu ma ga Hausawa tare da …. Su ne ‘ya’yan ne na Hausawan da suke daure aure da mataryen Jukunawa. Yawancin wadannan Musulmi ne, amma tafarkin asali na Jukunawa da Tivi da ….. tsafi ne An san sarkin Jukunawa da sunan Aku Uka, sarauta ce mai zurfi kuma da daraja.

Farkon zuwan Bishara a garin Wukari daga hannun Sudan United Mission (SUM) ne. Su ne Turawan kasar Ingila, wato ‘yan’uwan Turawan masu mulkin danniya ke nan. Amma bukatar yada Bishara ta fi karfinsu har suka aika da shugabansu Dr. Karl Kumm don ya nemi abokan aiki a kasashe dabam dabam har kasashen Kanada da Amirika inda suka sami Christian Reformed Church (CRC), wata darika ce da tana bin koyarwar John Calvin. “Yan’uwa ne na su Presbyterian daga kasar Scotland, wato arewa da kasar Ingila. Su SUM Ingila suka danka aikin Bishara a kasar Wukari a hannun CRC, amma karkarshen tutar SUM ne suna aikinsu.

Aikin yada Bishara a kasar Wukari ya soma karkashen ‘yan Ingila, kuma a cikin jihar Arewa a lokacin da Nijeriya ke a jihar guda uku ne kurum. Farkon sunan darikar da ta tashi a Wukari shi ne EKAS Benue. “EKAS” tsohon suna ne na kowane membar kungiyar TEKAN. Amma daga baya Gwamnatin Tarayya ta dinga kafa sabobbin jihohi. Wukari ta shiga sabuwar jihar North East, wato Arewa ta Gabas. Sunan “Benue” bai dace da darikar din yanzu ba, domin ba ta cikin sabuwar jihar Benue. An sake raba jihar. Yanzu kasar Wukari ke cikin jihar Gongola. Sa’anan cikin jihar Benue-Plateau har zuwa jihar Taraba, wanda ke sunan jihar din ke nan a yanzu. Saboda haka darikar ta nemi suna da ba a bukatar canjinta kowane loton da ake sake sunan jihar. Dalilin ke nan da aka zabi sunan CRCN, ba sunan jiha a ciki. Daga nan gaba ta huta da canjin sunayenta. CRCN ta kafu. Daga nan gaba ba za a yi maganar wadannan sunaye kuma ba, amma na takaita tarihin din nan domin in wani ya zo binciken tarihin darikar CRCN, ya kamata ya san yawan sakewar da aka yi a sunayenta da kuma da mishan nasu.

Amma a gane cewa ko da yake takardar nan ke zancen tarihin Bajukun, mutumin Wukari, ba a kafa hedkuwatar darikar a Wukari ba, amma a garin Takum, kusan kilomiter 80 kudu da Wukari. A lokacin garin Takum ke cikin Local Government na Wukari. Dalilin da ba a kafa hedkuwatar CRCN a hedkuwatar Local Government ba ke nan domin mutanen Takum suka karbi Bishara da zuciya daya fiye da mutanen Wukari.

*Asalin Habila Adda*

**Uban Adda Angyu shi ne Angyu Ice wanda ke da wani matsayin sarauta a garin Wukari. Gidansa a bakin kasuwa ne. Mahaifiyar Addan kuwa Bitiri ce, wadda ita ma aka haife ta a Wukari, amma asalinta Rafin Kada ne, wajen kilomita 20 a hanyar Takum. Ba a san shekarar haifuwar Addan sosai ba, sai dai a zamanin Aku Uka Agbanshu, uban Atoshi. Iyayen Adda matsafa ne. Kuma ba su yarda da wani tafarki ba sam, ko na Kirista ma fa. Tsafi ya biya masu bukata, ba ruwansu.**

**Loton da shi Addan ke cikin yarontakarsa su mishanari na kasar Ingila, wato su SUM na asali, suka kafa wata makaranta a garin Wukari mai suna "CRI." Ma'anar sunan kuwa da Turanci "Christian Religious Instruction" ko kuwa "Makarantar Koyar da Addinin Kiristanci." Makarantar tana cikin garin daidai inda daga baya aka gina majami'a ta fari wadda ke dub da sabuwar majami'ar yau wadda aka bude ta a shekarar 1966, shekarar farkon zuwana a kasar Nijeriya ke nan.**

**Mallam Iliya Gani ke koyarwa a makarantar. Shi dan Wukari ne wanda ya ji Bishara daga bakin Mallam Maxwell, wani mutumin Ingila A Wukari an fi san shi da suna "Langa-Langa" domin shi dogo ne da tsire. Shi daya ne na cikin su mishianari guda hudu na SUM wadanda suka isa a garin Ibi a cikin jirgi na kogin Benue a shekara ta 1904. Mafarin SUM ke nan a Nijeriya. Shi Maxwell din nan da matarsa suka haifi wasu yara a Wukari. Daya daga cikinsu, namiji ne, ya rasu a Wukari. Kabarinsa ke gindin wasu itatuwa a kabarin Kiristi a bayan majami'ar Roman a hanyar asibiti. Aka sa wani giciye na karfe a kabarin. Sun kuma haifi wata yarinya mai suna Kay. Da ta yi girma, ta kama aiki a hannun SUM a Gindiri. Ta taba zuwa ziyara a Wukari. Su iyayen suka riga mu gidan gaskiya. Daga bakinsa ne Mallam Iliya Gani ya karbe Bishara.**

*Tarihin Tubewar Adda*

**Ada Angyu saurayi ne a lokacin. Da shi da wani abokinsa mai suna Audu sukan zauna kusa da makaranta don su ji koyarwar M. Iliya. Ba da dadewa ba Audu ya shiga makarantar, amma Adda bai iya ba saboda iyayensu sukan ki, sukan hana masa. Sukan ki Kiristianci da dukan zukatansu. Ba dama su yarda dansu ya shiga irin wannan makaranta. Adda ya cigaba da zama a bakin makarantar don jin koyarwar. Cikin koyarwar din nan ya ji zance biyun da suka dame shi kwarai. Na fari, Mallam Iliya ya ce wanda bai tuba ya bar tsafi ba ran mutuwarsa zai shiga gidan wuta inda zai zauna a wurin har abada. Na biyu, Yesu zai dawo ba da jinkiri ba. Wanda bai yi shiri ya karbe shi ba, shi ma zai shiga gidan wutar.**

**Addan ya damu cikin zuciyarsa. Ashe, abin ya kai haka? Bishara ya zama masa abin tsoro ne kwarai da gaske. Da shi da abokinsa Audu suka yi shawara da juna da zurfi har zuke zartas cewa su bar boka da tsafi, su bi Yesus, komai ya faru. A loton nan ne ya fara shiga makarantar da kuma ya soma hallartar taron sujada masubi a majami'ar CRCN a Wukari.**

**A loton da Adda ya tuba masubi a Wukari ba su yawaita sosai ko ba. Lissafinsu tsakanin goma sha shidda da guda asharin ne kawai. Ban da Adda da kansa da abokinsa da kuma M. Iliya Gani, ga Mallam Yamusa Aji da matarsa Agiwakwa. Yamusan din nan matuki ne a hannun Turawan Mishan a Takum. Gidansa dub da majami'ar CRCN Wukari. Ga kuma Mallam Andarawus Agbu, mai gini, da Nadogara. Abin tausayi ne, ni, marubucin littafin nan, ban san sunan matayensu ba ban da na Adisa ,matar Adda, da kuma Agiwakwa, matar Yamusa.**

**Da jin labarin dansu Adda ya tuba ya shiga tafarkin Kirista, sai iyayensa suka soma masa tsanani da gaske. Suka hana masa abinci da abin sha. Yungwa ce ta kama shi ba kadan ba. Sa'anda yungwar ta fi karfinsa, sai Addan yakan tafi wurin M. Iliya wanda gidansa ke kusa da nashi. Da farko malamin yakan ba shi abinci da abin sha kyauta, amma daga baya**

**yakan ba shi aikin lada don samun dan kwabo. Ladansa kuwa wajen kwabo uku ne wanda ya sayi abinci da shi. Sai daga baya, da ganin tsananin ke cingaba da zafi, M. Iliya ya gayyace shi Addan ya tashi a gidan iyayensa ya kwana a gidansa. Adda ya gaya mini cewa, "Bana so in fada duka wahalar tsananin da na sha a hannun iyayena, sai dai in gode ma Baba Iliya kwarai da gaske saboda yawan gudummawar da ya yi mini a lokacin. Da ba dominsa ba, da mai wiwuwa ne ban cigaba da tafarkin ba. »**

**Habila bai iya tuna da shekarar da ya tuba ba, sai dai ya faru ne a sarautar Aku Uka Ammadu. Saboda haka yana tsammani ya tuba wajen shekara ta 1931. Ya yi shaidar din nan a hannun M. Iliya Gani da na M. Sambo wanda daga b aya aka nada shi Gara Donga. Donga wani gari ne wajen kilomita 40 kudu da Wukari. Ya yi shaidar bisa ga ka'idar ikilisiyar zamanin da. A lokacin ba a kafa gu-gu sosai ko ba, amma dattibai a garin Ibi da kuma a Donga da Wukari sukan hada kansu cikin matsayin shugabancin Kirista.**

**A loton ga wani Baturen Mishan a garin Ibi, wajen kilomiter 33 arewa da Wukari a bakin kogin Binuwai. Yawancin 'yan garin Musulmi ne, ba Jukun ba. Sunan Baturen kuwa M. Stanley. Stanley din ya zo wajen M. Iliya da rokon shi danka masa Adda don ya bauta masa a gidansa cikin matsayin boyi. A lokacin kuwa matsayin ke da daraja kwarai a wurin 'yan kasa. Shi Baturen da matarsa sukan yi iyakar anniyarsu su karfafa Adda ya shiga tafarkin da zurfi har ga cibiyarta, su zama iyayensa cikin Ruhaniya. Muddar ransa Habila bai manta da su ba.**

***Auren Adda da Adisa***

**Ko da yake Adda ya riga ya shaida sunan Isa Almasihu, kuma ya gane da Bishara saboda zurfin koyarwar da ya karba daga hannun iyayensa na ruhaniya, wato M. Stanley da matarsa, duk da haka ba a yi masa baftisma ko ba. Dalilin rashin baftismar kuwa shi ne a loton nan ba a**

**karban mutum baftisma sai dai ya yi aure, a ga irin kokarinsa. Dalilin rashin aurensa dai saboda zafin tsananin da ya sha a hannun iyayensa na jiki. Har illa yau ma ya rasa kudin aure.**

**Ga yadda sukan tafi da sha'anin aure cikin ikilisiya a wancan zamanin. Kudin aure ya kai wajen sule takwas cikin tsohon kudin fam na kasar Ingila. A lokacin sule takwas babban kudi ne wanda da kyar za a tattara. Da ba domin taimkon M. Stanley ba, da Adda da kyar ya yi aure. Amma tun da shi ke Baturen ya fitar masa da kudin aure, Adda ya auri matarsa, wato Adisa. Su biyu kuwa ba su rabu da juna ba muddar ransu. Wani pasta na SUM-CRC ne, wato Edwin Smith, mutumin Ingila, shi ne ya daure masu auren a garin Ibi, ba a Wukari ba.**

**A loton nan dai ba akan sa rigar aure iri na Bature kamar su fari ba kamar an saba yi a zamaninmu na yau. A'a, akan sa rigar al'adar Nijeriya. Sai daga baya ne aka fara yin amfani da rigar aure iri na Bature, amma ba domin zartaswar ikilisiya ba fa. Dattiban ikilisiya ba su taba zartas cewa dole a yi aure da rigar Bature a bikin ba.**

**Habila bai manta da tsananin wahalar da ya sha tukuna a daure masu aure ba, amma bai yarda ya fada tarihin ba. Ya ce, « Bai yi kyau in fade shi duka ba. Ni dai sai godiya ga Ubangiji Allah. Bakina ya kasa godiya a gaban Allah. Shi ne mai iko dukka. »**

**Shi Habila da matarsa Adisa suka haifi da namiji daya tak. Suka rada masa suna « Josiah. » Da ya yi girma ya shiga makarantar nas, kuma ya kama aikin din nan a hannun tsofuwar Jihar Gongola....**

***Baftismar Habila***

**Fasta Stanley ne ya yi ma Adda baftisma a ranar Kirismati na shekarar 1942. Shi ne loton da Adda ya karbi sabon suna, wato Habila, sunan da**

**aka fi saninsa da shi. Iyayensa ba su ci nasara da zafin tsananin da suka yi masa ba.  Ruhun Allah ne ya ci nasarar cikin ran Habila.**

## Babi na Biyu
## HABILA ADDA MAI YADUWAR BISHARA

***Ilimin Bishara da Darajarta***

**A bayan baftismarsa cikin sunan Isa Almasihu, Habila ya kebe kansa ga yaduwar Bishara.  Kuma bai huta da shan azaba sabili da tafarkin ba.  Wato ya cigaba da shan tsanani irin da Kirista na yau a Wukari ba su taba sha ba, balle su gane.**

**Ya kamata mu Kirista na zamanin yau mu gane da irin tsananin das u kakaninmu na ruhaniya suka sha dominmu.  Yawancinmu muka karbi Bishara araha, ba tare da tsanani ba.  Ga kuma yadda Kirista 'yan zamani ba muke girmama su kakanin.  Mukan mai da su mutanen da ne, jahilai marasa ilimi.**

**Gaskiya ce, Fasta Habila da matarsa Adisa ba su da ilimi ko satifikat mai daraja na makaranta, amma fa suna da wata hikima daga wajen Ruhu Mai Tsarki wadda ta fi darajar takarda zurfin ilimi.  Nasu hikima ce ta bada kansu, ta bautar da kansu.  Tasu hikima ta gina tushen ikilisiya da kuma ta haskaken jama'ar Wukari da kewayensu.  Yawancin masu ilimin yau dai nasu « ilimi » ne na cin jama'a, balle su talakawa.  Suna ginin kansu ne kurum da manyan gidaje a nan kasarmu har ma a waje.  Ina hikima cikin irin wannan halin ?  Ya dace mu na karne na 21 mu yi ma Ubangiji godiya da ya tanada wasu 'yan kasa ya kebe su su yada Bishara kamar shi Yohanna Mai Baftisma  wanda ya yi shelar zuwan Macecinmu.  Da ba domin Fasta Habila da irinsa ba da ya yiwu mu mutanen Wukari muna cikin duhun tsafi na da har yanzu.**

***Yada Bishara a Kasar Mumuye***

**Bayan baftismarsa shi Habila ya far bin M. Stanley cikin rangadin da yake yi wajen kasar Zing, wato Mumuye ke nan. Farkon tafiyarsa zuwa kasar Zing ya yi da jirgin ruwa mai injun, amma daga baya yakan tafi wurin da kafa daga Wukari zuwa Zing har da sauran kasar Mumuye. Hanyar daji ne fa wadda ta bi kusa da hanyar kwalta ta yau. Daga Wukari ta bi Bantaje haye da Kogin Donga kusa da Garage da Nyankwala. Daga Bantaje sai Kwararafa, tsohon garin Jukunawa, da Mutum Biyu zuwa Jalingo har garin Zing din nan. A mai da hankali ga irin tafiyar da yakan yi fa : ba da mota ko da babur ne ba, amma da kafa ! Ai, farkon yaduwar Bishara wajenmu ba wasa ba ne, sai da shan zufa da tsanani.**

**Kuma su biyu sukan bi kauyukan Mumuye dukka, sukan hau duwatsu domin su bi ko'ina jama'a masu duhu suke. Kada kowa ya ce bai ji Bishara a wajensu ba. Ga rahoton da Fasta Habila da kansa ya bayar batun yada Bisharar da shi da M. Stanley sukan yi a wurin:**

**Shi Fasta Stanley mai Bishara ne da gaske wajen 'yan dufu. A Zing da duwatsu kewaye da garin ba wurin da ba mu je ba, ba sau daya ko biyu kawai ba. A'a, sau da yawa a kowane wuri da kuma kowane kofar gidajen jama'a. Na iya tuna da wasu wurare kamar tun daga Lankaviri har da Kona. Su Jukunawa ne a wurin. Ga kuma zuwa Kpanti Nap da Kpanti Shawa da Mika da Kweji da Jinderi da Zandi da Zan da Dossa Lamman. Har yanzu ga Kogon da Bitako da Kakulu da Gogo da Tgako da Bubom da dai sauransu da yawa wadanda ban iya in tuna da su ba. Ba hutu, sai rangadi, sai wa'azi, sai shaidar Bishara ko'ina da kulayaumin.**

**A lokacin Mumuye ke da zafin hali iri na da. Idan D. O., wato Baturen mulkin dannniya na wurin, zai yi rangadi a kasar, sai tare da 'yan sanda kamar guda goma sha biyu, tukuna ya shiga kasarsu. Ban da su, ba dama ya tafi wurin saboda hatsarin zafin halin 'yan kasa a zamanin.**

**Habila bai iya tuna da wasu abubuwanda suka auku masu a kasar Mumuye ba, amma y tuna da wani abin tsoro da ya same shi a hanyar Yakoko. Gwamnati ta hana mutane tafiya zuwa Yakoko, amma Habila da Stanley ba su yi niyyar zuwan Yakoko din ba. Kawai sukan bi gidaje bi da bi a bakin hanya ba tare su kai Yakoko ba. To, a hanyar din nan wata rana su biyun nan suka gamu da wasu matsafan Mumuye tare da wadansu dodanni iri nasu. Ko zun zo da nufin tare ma masu Bishara hanya ne? Ba a sani ba. Ba wanda bai ji tsoron wadannan matsafa ba, ko Baturen mulki ma. Shi ne dalilin da suke so hana a kai masu Bishara ; hatsari ya yi yawa.**

**To, lokacin gaskiya ta kewayo ken an. Su masu dodannin me za su yi ma ma'aikatan Ubangiji Mai Runduma, Allah Mai Iko Dukka? Matsafan suka umarci Habila da Stanley su rabu da hanya, su bi wajen daji ne kurum. Saboda yawan gajiyarsa a ran nan shi Fasta Stanley ya hau doki ne, ba da kafa yake tafiya ba. Su biyu suka ki su rabu da hanyar. Sai su Mumuyen su ce ya sauka daga dokinsa, amma ya ki har yanzu. Sai ya daga bindigar da yake rangadi ta ita ya yi kamar zai harbe su Mumuyen. Da yarensu Baturen ya ce su ba shi wurin domin su ma'aikatan Ubangiji Mai Runduna su wuce. Sai m umuyen suka firgita da su duk da dondanninsu, suka sheka gudu zuwa cikin daji. Habila ya ji tsoron ransa kwarai da gaska sabili da kowa ke jin tsoron matasafan Mumuyen. Amma Ruhun Allah ya fi karfinsu, sun firgita, sun gudu. Masu Bishara kuwa suka cigaba da tafiyarsu kamar ba abin da ya faru.**

**A yau dai kasar Mumuye ya sake kwarai da gaske. Daga baya aka kafa wata ikilisya a wurin karkashen tutar SUM-EUB, wato Evangelical United Brethren. Su memba ne na TEKAN da suna EKAS Muri, wanda daga baya ya zama EKAN Muri. Biye da haka kuma suka hada kai da darikar Amirika mai suna United Methodists (UM). Hedkuwatarsu a Zing ne inda Bishop nasu ke da zama. A yau haka su UM suna tare da CRCN cikin TEKAN da kuma CAN ko kuwa Christian Association of**

**Nigeria. Kuma suna cikin Jihar Taraba tare da CRCN. Daya daga cikin fastocinsu ya hau matsayin Gwamna ta jihar, wanda an san shi da sunan Gwamna Jolly.**

***Zaman Masu Bi a Wukari***

**Fasta Stanley da matarsa sun jitu da shi Habila har suna kaunarsa. Ba su so su rabu da shi. Da kyar suka yarda masa ya koma gida a can Wukari ya ga lafiyarsu. Suka ba shi daman yin hutu a gida har wata uku.**

**Ashe, zaman masu bi a Wukari ba lafiya. Habila bai ji labari ba domin a lokacin tafiya daga Zing zuwa Wukari yakan dauki lokaci da kuma ba waya. Da kyar ake jin labarin juna. Masu bi a Wukari kima ne da kuma daga cikinsu kimar din nan wasu suka koma da baya. M. Iliya Gani ya fadi, ya bar tafarkin da nisa. Yamusa Aji ya tashi zuwa Takum don ya yi ma Turawan Mishan tuki a wurin.**

**Amma wasu suna nan suna bin tafarkin Isa da anniya kamar su Andarawus Agbu da Istifanus Useni da kuma Kefas Angyu. A lokacin Baba Edwin Smith, Baturen Ingili, mai hidimar Jibin Ubangiji ne a Wukari. Amma fa su kima ne kurum.**

***Karatu a Makarantar Bishara a Lupwe***

**Habila bai dade a gida ba. Ya tashi ya je Lupwe, kusa da garin Takum inda Baba Smith da matarsa ke da zama suna koyarwa a makarantar Bishara a wurin. Habila ya shiga makarantar. Su Smith din biyu suka yi ma dalibansu gudumawa kwarai da gaske ta wurin koyar da tafarkin da kuma a fuskar ka'idodin aiki cikin ikilisya. Habila ya sauka karatu a wurin a 11 ga watan Afril a shekarar 1944 a lokacin yakin Hitler. Ya**

**gode ma Smith da matarsa mai suna Nelle da dukan zuciyarsa har muddar ransa saboda koyarwar da ya samu a hannunsu.**

***Yaduwar Bishara a Kudancin Jihar Taraba***

**Da saukan karatu a Lupwe, Habila ya shiga hannun dattiban CRCN na Takum. Amma a lokacin sunan jihar "Gongola" ne da kuma sunan ikilisiya "EKAS Benue" ne. Sunayen dattiban a wurin su ne Baban Fasta Istifanus da Haruna Angyu da Bitrus Bako da Nuhu Giwa da kuma Hassan Nikin. A hannunsu ne Habila ya yi aikin Bishara ko'ina a kudancin Gongola. Ya je wurare dabam dabam kamar su Marunshe da Kashimbilla da Lufu. Sun kuma koma da shi zuwa Lupwe inda ya yi wata hudu da wa'azi.**

**Wata rana da shi da Baba Smith da uwargidansa Nelle sun kama hanyar daji zuwa kasar Kurmi. I, hanyar daji ne da shi ke ba hanyar mota ko ta babur samsam. Sai da kafa suka yi rangadinsu na wajen wata daya. Suka yi shagalin Kirismati a kauyen Galeya ne. Suna a Ashaku, kasar Kurmi, sai wani mugun ciwo ya kada Baba Smith. Ba likita, ba magani, ba taimako ko kadan, sai dai na Ubangiji Allah da ikonsa. Ba hanya zuwa Lupwe sai na daji. Yaya za ayi? Sai addu'a. Suna fama da ciwon har mako guda, sai Allah cikin alherinsa ya ji ya kawo masa sauki. Sai suka kama hanya su koma gida, suka isa lafiya. Washegari Habila ya tafi Wukari.**

**Ba da dadewa ba sai dattiban Takum sun sake aika da Habila tare da wani mai suna Nuhu Giwa su yi rangadi zuwa kasar Kurmi har wata daya. Suka bi kauyuka a bakin hanyar dajin dukkansu, ba su kyale ko daya ba.**

**Suka bi wasu kauyukan Icen da kuma wani na Chamba, amma sun manta da yaren kakaninsu, ba Chambanci a garesu. Mazamnan wadannan kauyuka suka kasa kunne ga Bishara da marmari kuwa. A**

**wasu wurare suka zo da tambaya: me za su yi da kayan tsafinsu? Habila da Nuhu ba su gaya masu kome game da zancen nan ba, ko shawara ma ba su yi masu ba. Sun ce kawai su 'yan kasa da kansu in sun tuba su ne za su zartas da abin yi. Daya cikin wadannan kauyuka ke da suna Nugbo.**

**Daga Nugbo suka kama hanya zuwa garin Kungana. Hanyar da dan nisa har sun kwana a hanyar. A loton garin Kungana dabam da Kunganan da mun sani a yau fa a hanyar Mararraba zuwa Beli. Kufan Kungana ke da ganuwa ke nan, wato tsohon gari ne kuma mai daraja. To, a hanya masu Bishara din suka sadu da sarkin Kungana. Ba su ji labarin zuwan juna ba. Amma sun gode da saduwa da shi sarkin domin wani sarki a hanyar ke so ya hana masu wa'azi, amma sarkin Kungana ya fi shi daraja, ya umarci wancan karamin sarki ya tattara jama'arsa don su kasa kunne ga Bishara. Sarkin Kungana ya gode masu domin sakon da suka yi ma jama'ar wurin. Da suka isa a garin Kungana, sarki ya rike su har kwana biyu, bai yarda su tashi a wurin da sauri ba domin jin Bishara ya gamshe shi kwarai. Wannan ya faru ne watan da shi Aku Uka Masa-Ibi na Wukari ya rigaye mu gida.**

**Daga Kungana Habila da Nuh suka kama hanyar gabas maso kudu. Suka gamu da mamnyan duwatsu da kuma kuramai masu duhu ainun. Ba hanya fa, ko na daji ba, babu, sai daji da kansa kawai. Tafiya a wurin said a kyar. Ga igiyoyin kurmi ko'ina suka tare masu hany. Ga kuma hawa da gangara daga safe zuwa yamma. Ai, gajiya kuwa ba kadan ba.**

**Ina sukan kwana a wasu wuraren masauki fa har yanzu bas u iya huta ba domin wurin ya yi masu datti kwarai, ya cika muni ainu. Kafin su shimfada tabamarsu sai suka shiga daji su tare ciyawa tukuna su shimfida a kai. A waje ne sukan kwana domin daki ya cika da kazanta. Ko abinci ma sai da dabara. Sau da yawa suka dafa abinci da kansu komai gajiyarsu. Duk da haka ba su huta a wuri daya ba, sai dai inda**

**Lahadi ya same su. Suka gamu da wasu mutane mai suna Fari. Daga can kuma suka gangara zuwa wajen Bente, gabas da Galeya.**

**Wata rana suka sauka a Gayyama a hanyar Baissa. A wurin gardama da tashin hankali tsakaninsu da 'yan garin ya auku masu. Su masu Bisharar da isowarsu a garin sai suka je suka gai da sarki. Sai sarkin ya ba da izinin kiran jama'a domin su ji wa'azin Bishara. Sarki da kansa ne ya yi shelar gayyatar jama'arsa duka domin su ji abin da ya kawo su bakansu. Amma wasu 'yan garin ba swa son wa'azin Bishara a wurinsu. Suka hau makwabtansu da fada ba domin komai ba, sai dai su dama hankalin kowa kawai don kada su kasa kunne ga jawabin Habila da Nuhu. Amma sarkin ya kwantar da hankalin jama'a har su biyu suka sami damar shaidar Bishara a wurin.**

**Daga Gayyama suka cigaba da hanyar Baissa cikin kasar Ndoro. A Ndafero, tsohon Tumbu, mutane guda tara suka tuba. Sabili da wadanan masu tuba guda tara dattiban Takum suka aika masu wani mai Bishara ya yi aiki a wurin. Shi ne Dawuda Efi marigayi, wanda daga baya ya zama fasta na CRCN Nyita, a hanyar Takum zuwa Marrarraba.**

**Su Manzannin Allah suka tashi a Ndafero suka nufi Ashuku da Naman Gangare da Naman Babba har suka kai wani wuri mai suna Akwatiri, wato tsohon sunan Abong ke nan. Wurin yana a bakin kogin Donga kan iyakar kasar Nijeriya da Kamerou, wajen kilomita guda 33 gaba da Baissa.**

**A wurin suka haye kogin domin su shiga kasar mutanen Baminda cikin kasar Kamerou. Wato suka bar kasar Nijeriya fa, suka fita waje da Bishara. Su Bamindawa sun riga suka ji Bishara daga bakin wasu masu Bishara na Kamerou, amma suka kasa kunne so sai ga wadannan 'yan Nijeriya. Suka yi alkawari cewa za su auna maganar da suka ji daga bakinsu. Ya kamata a mai da hankali a nan fa. Tun Ikilisiyar CRCN ba**

**ta kafu ko ba, masu Bishara nata sun riga sun fara shaida sunan Isa Almasihu a kasar waje !**

**Daga Baminda Habila da Nuhu suka kama hanyar gida, wato garin Takum ke nan. Suka bi wasu kauyuka kamar su Bugu da Abohu da Bissaula. A nan ne suka yi Lahadi. Sarkin garin da matayensa dukka suka zo su ji Bishara daga wadannan Manzannin Allah. Sa'anan suka tashi a wurin suka bi wajen Dogon Jigawa da Nyido da Garge da Tutuwa da Tati har suka kai Takum. Sun cika kwana 30 daidai umarnin dattibai na wurin.**

***Yada Bishara a Bissaula***

**Da shi ke 'yan garin Bissaula sun mai da hankali ga wa'azin Bishara, dattiban sun sake aika da Habila zuwa wuring, shi kadai, ya yi kwana goma ya dawo. Ya yi wa'azi a wurin da dukkan karfinsa dare da rana. Wata rana da ya gama wa'azin, sai wurin ya yi shiru tsit. Habila ya damu. Ko sun yi fushi ne ? Bai gane ba. Sa'anan wani dan kasa na wurin mai suna Chabye ya zo gun Habila da cewa, « Yau na tuba, na karbi Yesu. » Ya ce zai rabu da tsafinsa duk da al'adun duhu, ya bi Yesus Mai Cetonsa. Sai ya tashi, ya je gida, ya ciccire kayan tsafinsa duk, ya kawo su gaban Habila. Sai ya hura wuta ya kokkone su duka sarai. Wasu 'yan garin su ma suka bi gurbin Chbye suka kawo nasu kayan tsafi suke kone nasu. Wadanda suka tuba suke kone kayans sun kai guda takwas ne. Sarkin ya ga abin da ake aikatawa amma bai hana ba. Daga baya shi Chabye ya karbi sunan Uri'ah a loton da aka yi masa baftisma. Habila ya ce, « Lalle ne tuban da wadannan suka yi, aikin Ubangiji ne. Shi ne Ya juya su. « Mafarin ikilisiyar Bissaula ke nan.**

**Habila ya koma Takum don ya ba da rahoton wa'azinsa. Dattiban sun yi farinciki da gaske, har suka zarta su aika da wani mai Bishara zuwa Bissaula ya zauma a wurin, yi aiki. Suna ta nema, suna ta nema. Ashe, babu wani mai bisharar da za su aika ? Wurin daji ne sosai fa a lokacin.**

**Ga manyan koguna da kuramai masu firgitar da masu tafiya. Duk da haka dai bai kyautu a bar su sabobin tuba su kadai ba mai koyad da su ba.**

**Sai suka kira Habila cewa ya tafi ya yi masu aikin Bishara a wurin. Ya yi masu biyayya; ya yi shirin tafiyar wurin. Da jin labarinsa, sai masu bi na Bissaula suka yi farinciki har suka zo gun Habila a Lupwe don su kai shi garinsu, da shi da matarsa Adisa da kayansu. Sun lura da shi yadda ya kamata. Sun biya masa dukan bukatarsa. Ya yi aiki a wurin shekara hudu ne, wato daga 1946 zuwa 1950.**

**Amma bai yi aiki a Bissaula kadai ba fa. Ya je wasu wurare a kewaya kamar su Abohun da Bubu har zuwa Ko'o a inda babban kotunsu ya ke a lokacin. Hanyoyin masu wuyar bi da gaske; sai wanda ya gani. Ga hawan duwatsu. Kuma ga wani kogin da za a haye sau tara rukuna a game ketarewarsa!**

**A 1950 Habila ya tashi a Bissaula. Ba wai an gama da aikin Bishara a wurin ba, amma domin wani mugun ciwo ne ya kada shi. Ya koma Lupwe don ya warke a wurin, ya sami karfi. Ya dade kafin ya warke ya sami sauki, amma sa'anda saukin ya zo, Habila ya cigaba da aikin yada Bishara, amma ba a Bissaula ba. Jama'ar Bissaula dai ba su manta da aikin da su Habila da Adisa suke yi masu ba. Balle shi mai baftisma na fari a wurin, wato Uri'a, ya tuna da shi har muddar ransa da godiya mara matuka.**

***Kulla da Yara a Makaranta***

**Sa'anda Habila ya some samun karfi, sai manya suka yi shawara inda za su aika da shi. Ga bukata a wurare dabam dabam—Ibi, Fikyu, Suntai, Rafin Kada? A shirye yake ya tafi inda dattibai suka zartas. Sun zabi Rafin Kada ne, a hanyar Takum zuwa Wukari. A tuna fa, ba hanyar kirki, ba motoci. Baba Smith ya ji tausayen Habila saboda yawan**

**tafiyarsa da kafa. Sai ya ba shi aron kekensa. Ya tafi Rafin Kada da keken, ya duba don ya gane da irin zama a wurin, sa'anan ya dawo Takum, a gama shawara.**

**Ashe, keken ya bace. An shiga gyara, amma da shi keken ya riga ya gaji ya kara bacewa. Tushen val ya tsinke gaba daya. Habila yana shiru kawai, ya rasa abin yi domin a loton kuwa kayan keke da wuyar samuwa da kuma da tsada ainu. Yaya za ayi? Baba Smith yana tambaya cewa ko Ubangiji bai nufe shi tafi Rafin Kada ba ne?**

**Su biyu sun a cikin shawara haka, sai Baba Fasta Istifanus da Fasta Jonathan Wamada suka same su biyu din nan cikin shawawararsu. Ko ya yiwu su bar zancen Rafin Kada, Habila ya zauna a Bika Gaba ya lura da yaran makaranta a wurin? Baba Smith ya yarda amma yana so ya ji ra'ayin Habila da kansa, ba ya so a tilasta shi yi aikin yara, aikin da bai saba da shi ba.**

**Habila kuwa bai cika son aiki irin wanna ba, amma ya ji tausayin manya. Suna ta neman mai kula da yaran wata nawa ne amma ina? Ba wanda ya kawo kansa. Wasu ke cewa aiki ne mai wuya. Wanda ba saba ba, sai da kyar. Ga shi kuma wurin a daji yake, ba a cikin gari ba. Ga kuma ladan aikin kima ne, bai isa domin biyan bukatar iyali ba. Da jin wadannan maganganun da kuma ganin bukatar aikin sai Habila ya yarda ya tafi ya zauna a wurin. Manyan kuwa suka koma Takum da farinciki da godiya sabili da suka sami mutum, bukatarsu ta biya ke nan.**

**Gidan yaran makarantar kusa da Bika Gaba yake, amma cikin ciyawa ko daji. Yara suka zo daga wurare dabam dabam kamar su garin Takum da kansa kuma daga wasu kauyuka kamar su Fikyu da Kpambai da dai sauransu. Iyayen yaran suka zo su gina ma yaransu dakunan kwana har zun kai guda shida. Sauran ginin dakuna da gyare-gyare suka bar a hannun yara da kansu. Sa'anda Habila ya kama aikin yara**

**sun kai wajen 36, amma sun karu har a shekarar 1950 sun kai kusan 100. Ai, aiki da yara masu yawa haka aiki ne mai wuya, sai wanda ya taba tukuna zai gane. Amma Habila ya gode ma Ubangiji don hankuri da karfin halin da Ubangiji ya ba shi ya biya bukatar yaran.**

**Sai ka ce aikin bai isa ba. Manya suka kara masa aiki. Ko da yake aikin yaran cikakken aiki ne, mai wuya kuma, suka kara masa aiki dabam dabam. Sun danka masa majami'ar Sabon Gidan Lissam kafin suka sami mai Bishara nasu na kansu. Sa'anan suka danka masa lura da masu bi a Bika Gaba. Bugu da kari ya rika zuwa makarantar firimari na En'e a garin Takum ya koyar da addini a wurin sau biyu a mako, wato ranar Talata da ta Juma'a ke nan. Da farko dai yake tafiyar wadannan wurare da kafa. Sai daga baya ya sami keke nashi na kansa. Lalle ne fa samum keken ya taimake shi ba kadan ba, ya rage masa nauyin tafiye-tafiyensa. Habila ya gode ma Ubangiji saboda keken kwarai.**

***Aikin Fasta a CRCN Wukari***

**A shekarar 1955 ne aka bude makarantar fastoci a Lupwe. Habila ya shiga makarantar tare da wasu manya shugabannin sabuwar ikilisiya da ta tashi a ko'ina. Za a iske labarin wadannan fastoci a kasa bayan da aka gama da tarihin aikin Habila da kansa. Suka sauka karatu a shekarar 1957. Wato kos ne na shekara biyu da kuma da Hausa ne, ba Turanci ba. Masu jin Turanci kima ne a zamanin.**

**Sunayen sauran dalibai a makaranta da kuma sunayen gu-gu inda daga baya aka nade su fasta su ne:**

| | |
|---|---|
| **Baba Fasta Jonathan Wamada** | **Takum** |
| **Fasta Bulus Kwashe** | |
| **Fasta Sule Bete** | |
| **Fasta Dawuda Efi** | **Nyita** |
| **Fasta Bulus Inashi** | **Donga** |

| | |
|---|---|
| **Fasta Musa Ciroma** | **Bika Gaba** |
| **Takum** | |
| **Fasta Iliya Abowa** | **Ashuku, Abong** |
| **Bakundi, Baissa** | |
| **Fasta Nuhu Panciri** | **Ndafero, Serti** |
| **Fasta Daniel Ndeyatso** | **Lissam, Takum** |

**Wadannan fastoci na CRCN na fari suki cika harkokin matsayinsu, suka biya bukatar sabobin tuba dubu dubai da anniya da gaskiya.  Allah ya ba su ladansu.  Amin**

**Da ya sauka karatun a 1957, sai Habila ya koma gida a Wukari.  Su dattiban CRCN Wukari bad a bata lokaci bad a ganin dan'uwansu ya gama makarantar fasta sai nan da nan bayan mako biyu suka mike masa takardar kiran fasta bisa ga al'adar CRCN a lokacin.  Bayan da ya dauki mako biyu domin addu'a da tunani don ya tabbatar da kiran da aka yi masa, sai ya amsa, ka karbi kiran.  A 2 ga watan Maris na 1958 ne aka shafe shi fastar CRCN Wukari. Fastocin da suka sa masu hannun shafewa su ne fastocin Turawan Mishan, wato Fasta Peter Dekker wanda ke zauna a tashin mishan a Wukari a lokacin, da kuma ga Baba Smith da shi Fasta Robert Recker.  Dan kasa cikinsu fastocin shi ne Fasta Jonathan Wamada wanda ya yi makaranta tare da Habila amma aka shafe shi ran Lahadin da ya wuce.  Jama'ar Kirista daga wurare dabam dabam suka hallarci wannan bukin shafewar Habila, wato daga Donga, Takum da Baissa, har ma daga NKST a Zaki Biam, wato darikar Tivi ke nan.**

**Dattiban CRCN Wukari wadanda suka gayace Habila ya zama nasu fasta su ne:**

**Baba Andarawus Agbu**

**M. Istifanus Useni**

**M. Kefas Angyu**

**M. Solomon Ahima**

**M. David Bako Agbu**

**M. Samu'ila Gani**

**M. Ibrahim Sangari Usman**

**Tun lokacin, Andarawus Agbu da Solomon Ahima da David Bako suke rasu cikin tafarkin Kirista. Useni da Angyu suka kauce daga tafarkin. Samu'ila Gani ya zama Permanent Secretary na Gwamnatin Tarayya. Daga baya kuma aka zabe shi Deputy Governor na Jihar Taraba a karkashen Gwamna Jolly. Yanzu yana hutu tsakanin Jos da Wukari. M. Ibrahim Sangari da kafin soja sun dauki mulki, an nade shi wasu manyan matsayai a hannun Gwamnatin Tarayya. Kuma yana cikin manyan dariktan wani kwampanin mutanen Netherlands. A yanzu haka ya maida kansa bishop ne na wata darika dabam a Wukari.**

**Ko da yake Habila shafaffen fasta ne na CRCN Wukari, amma aikinsa bai tsaya a wurin ba ko kadan. Aka danka masu masu bi a ko'ina a kasar Wukari. Har yanzu ba hutun rangadi da na tafiye-tafiye, amma yanzu da keke ne inda da hanyar keke, ba da kafa ba. Wurin aikin sabon fastar din kuwa ke da fadi ainun, wato daga Akwana a bakin kogin Katsina Alla zuwa Rafin Kada a hanyar Takum zuwa Tsokundi da Nyankwala a bakin kogin Donga har Jibu da Ibi a bakin kogin Binuwai. Kuma har yanzu bai rabu da hatsari iri-iri ba. Wata rana da shi da Fasta Dekker ke tafiyar Dampar haye da kogin Binuwai. Saura kadan wani dorina ya kashe su.**

**Ko da yake a lokacin masu bin Isa ke karuwa da sauri, tsananin masu bi a hannun matsafa kamar su iyaye da kuma wasu sarakuna bai tsaya ba. Misali a shekarar 1963 Shaidan ya zuga jama'ar Adikenda su kone majami'a inda Kirista na garin ke yi ma Ubangiji Allah sujada. Ni mai walafa tarihin din nan, wato Baturen Mishan Fasta John ko kuwa Yohanna Boer wanda ya zauna a Wukari daga 1966 zuwa 1974, bayan da shi Fasta Dekka ya koma kasarsa, wato da shi da Fasta Bulus Inashi daga Donga muka tafi wani kauye a bakin kogin Taraba inda 'yan gari su**

**kuma suka kone majami'ar masu bi a wurin. Fasta Bulus yana so ya ba sarkin wurin tsoro. Ya gaya masa ya zo da wani babban Bature wanda kasar duka ke a hannunsa. In an sake kone majami'ar Kirista, shi Baturen zai dawo ya san abin yi! Ni Boer kuma ina koyarwa a CLTC inda aka koyad da shugabannin ikilisiya, balle masu bishara. Su 'yan makarantar sukan zo da labaran tsanani iri-iri da su matsafa ke yi ma Kirista ko'ina. Ya kamata mu gode ma Ubangiji yadda yanzu ga sulhu da salama tsakaninmu da su, amma a lokacin fa ba sulhu ko salama ko da jituwa, balle cikin kauyuka. A lokacin ba gardama tsakanin Kirista da Musulmi ko.**

**Allah Mai Iko Dukka Ruhunsa ya yi aikin al'ajibi a kasar Wukari. A shekara ta 1966, CRCN Wukari ta bude sabuwar majami'a wadda ta kunshi mutane fiye da 800! Cikin dukan fadin kasar kewaye da garin Wukari inda Fasta Habila ya yi rangadi da Bishara masu bi kima ne. Lissafinsu a lokacin ya kai 85 ne kadai. A shekarar da aka wallafa wannan littafi da farko, wato 1984, sun kai wajen 4,000. A yanzu haka nan a 2011 sun kai….** Lalle ne kuwa, al'ajibi ne da gaske.**

**Fasta Habila ya lura da wadancan wurare duka zuwa lokacin da aka sami wasu fastoci. Amma kafin sun iya kiran fasta su dauki nauyinsa da bukatarsa duk da na iyalinsa, sai a kafa su gu tukuna su yi zaman kansu ba karkashen gu na Wukari ba. Ga su gu-gun da aka kafa su da kuma shekarar kafawarsu :**

| | |
|---|---|
| **CRCN Bege a Suntai—24 ga Fabrairu, 1963** | |
| **CRCN Rafin Kada** | **24 ga Janairu, 1965** |
| **CRCN Nyankwala** | **14 ga Maris, 1965** |
| **CRCN Ibi** | **????** |
| **CRCN Tsokundi** | **20 ga Janairu, 1971** |

**Wadannan gu suka dinga karuwa har su ma aka raba su don a dinga kafa sabobin gu a kasar Wukari. A yau haka ga gu guda ....** a wurin.**

**Ga kuma su sabobbin fastocin da suka hau kujerar Habila. Na farko, Fasta Ezekiel Nyajo ya dauki nauyin CRCN a garin Ibi, amma bayan da ya yi aikin din nan har fiye da shekara 20, sai ya kauce, ya musulunta. Su gu na Bege suka dauki wani sabon fasta wanda ya sauka karatu at TCNN, kusa da Jos, wato David Gani Angye, suka nade shi fasta nasu. Sai Fasta John Boer, mawalafin takarda nan, ya zo daga kasar Kanada ya dauki nauyin Rafin Kada da na Nyankwala. Ya na hidimar fasta a wadannan gu-gu, amma nauyin aiki na kowace rana ke a hannun manyan masu bishara a wurin, kamar su M. Istafanus da M. Iliya Danjuma. Daga baya aka nade wani mai bishara mai sunan Filibus Aboki ya kama aikin fasta a gun Nyankwala. A lokacinsa M. Iliya ya tafi makarantar fasta. Sa'anda Fasta Aboki ya tashi a Nyankwala, suka shafe shi Iliyan fasta nasu. Haka ma a gun Rafin Kada. Fasta Boer yakan yi masu hidimomin fasta, amma M. Ifraimu Nyajo ya dauki nauyin aiki a wurin zuwa lokacin da aka sami wani sabon fasta dan kasa mai suna Bitrus Angyunwe, wanda daga baya ya shiga soja ya yi masu aikin fasta cikin rundunarsu. Fasta Habila da kansa ya cigaba da matsayin fasta a gu na Wukari har zuwa lokacin da aka yi masa ritaya a 1983. A lokacin nan kowane gu inda ya yi aikin fasta a kasar Wukari duk suna da fasta dan kasa nasu.**

**Yabo ya tabbata ga Ubangiji domin Bishara ta kafu sosai a kasar. Fasta Habila ya gama aiki nasa, ya huta. Gu na Wukari suka gina masa gida mai dacewa domin shi da matarsa Adisa su huta da gajiyarsu. Wani sabon fasta mai sunan Ishaya Bako wanda ya yi karatu a TCNN ne ya hau kujerarsa na fasta. Habila ya riga mu gida a shekara ...** ; Adisa kuwa a shekara …** Allah shi ba da lada ga wadannan bayi nasa wadanda suka bada da kansu gareshi da dukan zukatansu shekara da shekaru.**

***Don haka sai ku karbe shi da matukar farin ciki saboda Ubangiji, kuma ku girmama irin wadannan mutane, don ya kusa ya mutu***

***saboda aikin Almasihu yana sai da ransa don ya cikasa dawainiyarku... (Filibiyawa 2 :29-30).***

**Amin da amin !**